# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Ista ta farko



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Lyn Doerksen**

**Fassarawa: Maren Dameng Daniel**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2020 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**

Wata mace ta tsaya a gefen tudun waje mai hayaniya, idanunta jajaye ta ɗago shi tana ganin abin baƙin ciki da ke faruwa. Ɗan ta ya na mutuwa. Wannan maman ita ce Maryamu, ta tsaya kusa da wurin da aka giciye Yesu a kan giciye.





**Yaya akayi dukkan waɗannan abubuwa suka faru? Ya ya Yesu zai gama kyakkyawan rayuwan sa ta wannan mummunan hanya nan? yaya Allah zai amince a kafa wa ɗansa ƙososhi a kan giciya yamutu a can? Yesu ya yi kuskure akan ko wanene shi? Allah ya yi kuskure ne.**



**A'a! Allah bai gaza ba. Yesu bai yi wata kuskure ba.  Yesu kullum ya na sane da cewan wanna rana za'a kashe shi ta hanyan magunta na mutane.  A lokacin da Yesu ke karami, wani tsoho mai suna saminu ya fada wa Maryamu cewan bakin ciki na gaba.**



**Kwanaki kaɗan kafin a kashe Yesu, wata mata ta zo ta saka wa sawun ƙafan Yesu mai mai tsada da kamshi. “Tana ɓata kudi’almajirai sun yi guna-guni.” Ta yi aiki ne mai kyau “Yesu yace. Ta yi ne don bisona.” Wata baƙuwar zance ne wannan!**


**Bayan wannan, Juda, ɗaya daga cikin almajirai goma sha biyu na Yesu, ya yarda zai ci amanar Yesu wa babban limami akan azurfa 30 talatin.**





A wurin bikini din ƙetare na
Yahudawa, Yesu ya ci abinci
na ƙarshe tare da almajiransa.
Ya gaya musu abubuwa masu
kyau game da Allah da kuma
alƙawuransa ga kuma ƙoƙo ya
ce su sha, wannan ya zama tuni
cewan naman jikin Yesu da
jininsa an bayar don
ya kawo ceto
da gafaran
zunubai.

**Sai Yesu ya faɗa wa abokansa cewan za’aci amanar shi kuma za su gudu ‘ni bazan gudu ba' in ji bitrus Yesu ya ce’ kafin zakara ta yi cara, sau uku zaka yi musun sani na.**





A cikin wancan daren, Yesu ya tafi tudun lambun Gastamani. Almajiran da suke tare dashi su ka fara bacci. “Ya Ubana,” Yesu ya yi adu’a ga Allah’ Ba nufi ƙoƙon ya wuce daga gareni. Amma ba yadda ake nufin ba amma yadda kake nufi .


Ba juma ba sai wasu jarumai suka shiga
cikin wurin addu’an sai Bitrus bai tsaya
wata-wata ba ya yanke kunnen wani
mutum, Yesu ya taɓashi sai ya
warkas dashi.  Yesu ya sani
cewan tsare shi da akayi
don kama shi yana
cikin shirin Allah.



Waɗannan sojojin suka kai Yesu gidan babban limanin. A can shugaba na yahudawa yace Yesu ya mutu. A kusa da wurin wutan jin ɗumin bayin sarki ne Bitrus ya tsaya. Sau uku mutane suna cewa Bitrus, cewan “kana tare da Yesu” Bitrus ya yimu su kamar yadda Yesu ya fada zata faru. Bitrus ya la’anta da kuma rantsewa.




COK-A-KOOKORI-KOO



**Ba a jima ba sai zakara ta yi cara. Ta zama kamar muryar Allah ne zuwa ga Bitrus ya tuna kalmomin Yesu sai ya yi kuka mai tsanani.**



Juda bai sami kwanciyar hanka liba. Ya san Yesu baiyi laifin kome ba ko zunubi ba. Juda ya dauki wannan azurfa 30 talafin ya mayer wa babban limanin, amma Limamin ya ki karbar azurfan.



**Juda ya ajiye azurfan a kasa, ya fita ya je ya rataye kansa.**




Babban limamin ya kawo Yesu gaban mahukunta, wato Gwamnan Roma, sai mai hukunci ya ce, “Ban ga wani laifi akan wannan mutumin ba amma Jamaa” suka rika cewan “a giciye shi! A giciye shi!”

**A ƙarshe gwamnan ya mika Yesu, ya kuma sa hannu a takarda don yin kisan Yesu a kan giciye. Sojoji suka soki Yesu, sun tofa masa miyawu a fuska, suka yi masa bulala. Sun yi masa rawanin kaya suka danna masa a kai, sai suka buga masa kusa a kan giciyen katako ya mutu.**



Ko yaushe Yesu yana sane cewan irin mutuwar da zai yi kenan.  Ya kuma sani cewan mutuwarsa za ta kawo gafaran zunuban wadanda suka gaskata da shi.



Barayi biyu ne aka giciye su tare da Yesu.  Daya ya gaskatta Yesu ya tafi aljanna ba sai dayan ya ki gaskatawa.



**Bayan awowi na wahala, sai yesu ya ce “yaƙare” sai ya mutu.  Aikinsa yaƙare. Abokansa suka binne shi a kabari.**

Sai sojojin Romawa suka rufe kabarin suna gadi don kada wani ya shiga ko ya fita daga kabarin.



**Idan wannan ne karshen labarin, wane irin bakin ciki ne zai zama.  Amma Allah ya yi wani abin mamaki. Yesu bai zauna a mattatu ba!**



Rana ta farko a mako da sassafe, wasu almajiran Yesu suka ga an ture babban dutse daga kabarin Yesu.  Da suka duba ciki, suka taras Yesu baya a cikin kabari.



**Wata mata tatsaya a bakin kabarin tana ta kuka. Sai Yesu ya bayyana mata! Da farin ciki ta tafi taje ta fadawa sauran almajirai "YESU YANA DA RAI! YESU YA DAWO DAGA CIKIN MATATTU!"**



**Bada jimawa ba Yesu ya zo gun almajirai, sai ya nuna masu hannunsa da kafansa da aka kakkafa ƙusa akai. Gaskiya ne YESU NA DA RAI KUMA! Ya gafarci Bitrus don ya musance shi, ya gaya wa almajiransa su gaya wa dukan mutane game das hi. Sai ya koma zuwa cikinsama wurin day a fito a ranar kirismati ta farko.**

# Ista ta farko

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Matta 26-28, Luka 22-24,**
**Yahaya 13-21**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin
Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi.  Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai.  Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu.  Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama.  Idan ka bada gaskiya ga Yesu.  Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe.  Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi.  Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada.  Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka.  Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin.   Yahaya 3:16